# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Daniyel Kamamme




**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Jonathan Hay**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**



**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**




**Daniyel da abokansa uku suna zama a Isra'ila. Wata rana wani babban sarki ya zo garinsu ya kwashe duka 'yan mazan da suke da wayo zuwa garinsa. Sarkin yana da dogon suna – Nebukadnezar- kuma yana zama a wani kasa mai nesa mai suna Babila.**



**Ba a wulakanta wadannan ‘yan mazan a Babila ba. Sarki ya riga ya zaba mafi wayo daga kowane kasa a duniya. Nufinsa shi ne ya horar da su a yaren Babila don su zama ‘yan hidimarsa don taimake shi ya gudanr da ayuukan mulkinsa.**



3

**Abincin yana da kyau, kuma. Yan mazan suna ci duk abin da sarki yake ci. Amma Daniyel da abokansa ba sa so su ci abincin saboda an riga an mika shi ga allolin karya. Daniyel ya riga ya yi alkawari cewa ba zai taba yin wani abu wanda Allah ba ya so ba. Allah na Isra’ila ya riga ya umarta mutanensa kada su hada kansu da gumaka ko allolin karya ba.**



4

**Daniyel ya nemi izini daga mai lura da horarwarsu domin kada ya ci abincin sarki. Idan har sarki ya ji, ba zai ji dadi ba. Amma Allah ya riga sa Daniyel yana da farin jini a gare wannan mutum.**



5

**Ya yarde ya ba Daniyel da abokansa wani gwaji. Za su yi kwana goma suna ci ganye da ruwa kawai. Bayan kwana na goma sai Daniyel da abokansa sun fi saura ‘yan mazan da suke ci abincin sarki lafiyar jiki. Sai aka bar su su ci gaba da ci ganye da ruwa.**



6

**Wadannan saurayin sun daukaka Allah. Allah kuma ya daukaka su. Allah ya ba su sani da gwaninta a kan abubuwan da suke koyo, ai Daniyel ya kasance da hikiman gane ru’uyoyi da mafarkai.**



7

**Bayan shekaru uku na makaranta a Babila, duka ‘yan mazan nan aka mika su ga Sarki Nebukaddnezar. Ya dauki Daniyel da abokansa uku a matsayi mafi duka da sauran. Da gaske, Sarki ya gane cewa Daniyel yana da hikima fiye da duka maza masu hikima na mulkinsa.**



8

Wata rana da daddare, sarki ya yi mummunan mafarki. Sai ya kira duka masu dubbansa, masu karanta taurari, bokaye su zo su tsaya a gabansa. Sarki ya ce, “Na yi mafarki, kuma ruhuna yana marmari ya gane ma’anar mafarkin.” Masu hikiman suka amsa, ‘Ya sarki, ranka ya dadde! Gaya wa ‘yan hidimarka mafarkin, za mu kuwa gaya maka abin da yake nufi.”



9

Sarki ya amsa, “A’a! Dole sai kun gaya mini abin da na yi mafarki a kai da ma’anarsa. Idan ba ku yi ba, za a yayyanka ku gidajenku kuma za a kokkone! Amma idan kun gaya mini mafarkin da ma’anarsa,” sarki ya ci gaba da magana, “za ku karba jyautayi da lada da babban daukaka.” Tabas, babu ko dayansu wanda ya iya fada wa sarki mafarkin.



10

Masu hikima na sarki suka gaya wa sarki, “Babu mutum a duniyan nan wanda zai iya yin abin da kake ce wa mu yi. Alloli ne kadai wanda za su iya yin wannan, kuma ba sa zama a duniya.” Sai sarki ya yi fushi sosai. “A halakar da duka maza masu hikima a Babila.” Ya umarta.



11

Sa’ad da sojojin suka zo wurin Daniyel, ya ce wa Antiyok, shugaban sojojin sarki, “Don me sarki yana halakar da duka maza masu hikima?” Sai Antiyok ya gaya wa Daniyel kome da komen da ya faru. Daniyel ya tafi ya gan sarki. Sai ya ce a ba shi dan lokaci donya gaya wa sarki ma’anar mafarkinsa.



12

Sai Daniyel ya tafi gidansa, ya fada kome da kome wa abokansa Shadarak, Meshak, da Abednego. Daniyel bai sai mene ne mafarkin ko ma’anar mafarkin ba, amma ya san Wani, wanda ya san kome da kome. Wannan Wani shi ne Allah. Saboda haka, Daniyel da aboknsa suka yi addu’a.



13

Allah ya nuna wa Daniyel mafarkin da ma’anarsa. Daniyel ya albarkaci Allah na sama, yana cewa, “Albarka ga sunan Allah har abada abadi, gama hikima da karfi nasa ne.” Daniyel ya koma da sauri-sauri zuwa wurin sarki ya ce masa, “Akwai Allah a sama wanda yake bayyana atsirai.” Sai ya gaya wa sarki abin da ya yi mafarki a kai da ma’anar mafarkin.



14

**Sa'ad da Sarki Nebukadnezar ya ji mafarkin da ma'anarsa, sai ya fadi kasa a gaban Daniyel ya ce, "Da gaske Allahnka Allah ne na alloli, da kuma Ubangijin Sarakuna, da mai bayyana atsirai, tun da ka iya bayyana wannan asirin!" Sa'an nan sarki ya mai da Daniyel babban mutum, ya kuma ba shi kyautayi masu girma. Ya mai da shi mai mulki a bisan duka yankin Babila, da shugaba a kan duka maza amsu hikima Babila.**







**Daniyel Kamamme**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Daniyel 1-2**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**






31

60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**